# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da





# Nuhu da Ruwan Dufana

Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Tammy S.

Fassarawa: Maren Dameng Daniel

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2020 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.

Nuhu mutumi ne mai bauta wa Allah da sujada. Dukkannin sauran jama'a sun tsane shi kuma basu yin biyaya ga Allah. Wata rana Allah ya yi magani mai ban mamaki. “Zan halaka duk mugayen mutane da duniya nan,” Allah ya gaya wa nuhu. “Iyalen ka ne kaɗai za su tsira.”





**Allah ya faɗawa Nuhu zai aiko da ruwa wanda zai rufe duka duniya. “Ka sassaƙa baban jirgi wanda zai lya ɗaukan lyalan ka da kuma dabobi masu yawa ,” Allah ya umurci Nuhu. Allah ya faɗawa Nuhu yadda zai sassaƙa jirgin. Sai Nuhu ya fara!**





Mutane kuwa sun yi wa Nuhu ba'a yayin da ya gaya masu dalilin sa na sassaƙa jirgin. Nuhu kuwa ya ci guba da aikin sa. Kuma yana yaɗa bishara yana wa'azi akan Allah. Amma ba wanda ya ji shi.



Nuhu kuwa ya bada gaskiya mai yawa. Ya yadda da Allah duk da ruwan sama bai taɓa sauƙa. Bada bata lokaci ba jirgin ya kammala domin ɗaukan kaya.

Sai dabbobi suka zo. Allah ya kawo ire-ren dabbobi guda baƙwai, da biyu na sauran. Tsuntsaye manya da kanana, dabbobi ma kanana da dogaye suka kama hanya zuwa cikin jirgin.



Kodayake mutane sunyi ta ihu suna zagin Nuhu ya yin da yake shigar da dabbobi cikin jirgin. Basu daina zunubi wa Allah ba.  Basu kuma nemi izinin shiga jirjin ba.





A ƙarshe dukan dabbobi da tsuntsaye sun shiga cikin jirgin "shigo cikn jirgin" Allah ya gayyaci Nuhu "kai da iyalen ka." Nuhu, da matarsa, yaran sa uku da matansu suka shiga jirgin. Sai Allah ya rufe kofan jirgin!



Sai ruwan sama ya sauƙo. Wannan ruwan mai yawan gaske da aka yi ya jika duniya na tsawon kwana arba'in.



Ruwan ɗufanan ya watsu zuwa birane da kauyuka. Da ruwan ya tsaya, dukan tsaunuka sun shiga cikin ruwa. Kowane abu da yake numfashi sun mutu.



Lokacin da ruwan dufana ya cika duniya, sai jirgin yayi ta tafiya a saman ruwan.  Zai iya kasan cewa da duhu ko gargada ko abu tsoro. Amma jirgin ya tsare nuhu daga ruwan dufana.

Bayan wattanni biyar na ruwan ɗufana, sai Allah ya aiko da iskar guguwa mai bushar kasa. A hankali jirgin ya sauko daga tudun Ararat. Nuhu ya kasance cikin jirgin na tsawo kwana arba'in da yini arba'in yayin da rowan ya tsaya.



Nuhu ya fitar da hankaka da kurciya ta taga. Basu sami wurin da za su huta mai tsabta ba, sai kurciya ta dawo wurin Nuhu.



**Nuhu ya fitar da hankaka da kurciya ta taga. Basu sami wurin da za su huta mai tsabta ba, sai kurciya ta dawo wurin Nuhu.**



Bayan mako daya sai Nuhu ya sake fitar da kurciya. Kurciyar ta dawo da ganyen zaitun a bankita. Bayan wata makon Nuhu ya gane cewan duniya ta bushe domin kurciyar bata dawo ba.

**Ubangiji ya fada ma Nuhu cewan lokaci yayi da zaku fita daga wannan jirgin. Nuhu tare da iyalensa suka fitar da dukkan dabbobin daga cikin jirgin.**



Wane irin farin ciki Nuhu ke ji! Ya gina wurin ibada yayi wa ubangiji sujada domin yadda ya cece shi da iyalensa daga wannan ruwan ɗufana.





Ubangiji ya yiwa Nuhu alƙawari. Cewan ba zai sake aiko ambaliyan ruwa duniya ba domin zunuban ɗan Adam ba. Ubangiji ya bada babban tuni na alƙawarinsa. Bakan gizo shi ne alamar alkawaran ubangiji.


Nuhu da iyalansa su sake samun sabon rayuwa bayan ruwan ɗufana.
A ɗan lokaci zuriyan sa sun sake cika duniya.  Dukkan kasashen duniya, sun fito daga tsotson Nuhu ne da ‘ya’yansa.

# Nuhu da Ruwan Ɗufana

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Farawa 6-10

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130


KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**